# Yaya akayin renon iri mangwaro cikin leda ? Duabara ta daya (1)

Wanan dubara ita ce mafi saukin aikatawa. Ku tabbatarda cewa tun farko kwolayen mangwaronku basu lalace ba kuma basuda wata alama cige cige ko hunhuna, don gudun kada idan sunada ciwon su baza shi cikin fangalin.

1



Ku zabi tsaptatar leda wadda zaku huhudewa daga kasa da kewaye. Ku cika ta da hadadiyar kasa da takin galgajia. Wanna takin na iya zama tsimmame ko kuma garwayaye da kashin kaji ko wasu dabobbi can daban. Ku rinka ban ruwa daidai wadeda domin samun muhalli mai ni'ima.

2



Ku sa kwolon magwaron hanci kasa, kenan doron sama sai ku turbude shi cikin kasa ba tare da an nutsa shi ba sosai.

3



ku dinga bada ruwa kai a kai zaku ga dan mangwaron ya bubugo kuma yayi sayu cikin wata daya. Da zarar sayun sun huto, ya kamata a dasa shi.

**Texte** : Ibrahim Habi, Patrick Delmas, Florent Birchen, Zakay Yayé, Aïssa Kimba, Omar Djibo, Abdoul Baki Mahamane, Salamatou Sami, Mariama Habibou
**Photos** : Ibrahima Habi, Abdoul Baki Mahamane, Jamilou Saadou Idi —— **Conception graphique** : Jamilou Saadou Idi

Programme nigéro-allemand de Promotion de l'Agriculture Productive (PromAP)
GIZ/PromAP - BP 10 814 - Niamey, Niger